

Wasan Banza

Littafin karatu a sauƙaƙe - Mataki na 3

Hausa

Zuwa ga malamai da iyaye:

Kafin a fara amfani da wannan tsarin koyon karatu, dole sai ɗalibi ya: • San amon sautukan haruffan Hausa; • Iya gane kalmomin da aka saba da su.

Wasan Banza

Hausa Nigeria

Copyright © 2017, Enabling Writers Project - American University of Nigeria

http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/

http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/ An yarda ka yi amfani da wannan aikin ta wajen harkar kasuwanci. Kana iya ɗaukar aikin nan a yadda ya ke ko ka yi ƙari akai. Dole ne ka ajiye haƙƙin mallaka da kuma alaƙanta aiki ga marubuta, masu zayyana da sauran su. ISBN

Grace Malgwi Writing Trainer/Collection Editor

Prof Salisu Yakasai and Prof Lawan D Yalwa Hausa Language Consultants

Nas Yakubu Bloom Trainer

Story Writers Husaini Adamu; Adamu Babbikoi; Garba Mohammed Dantsoho; Jalauddeen Ibrahim Maradun; Yasalu Haruna; Muhammed Umar Deba; Idris Hamid; Ibrahim Baraya; Dahiru A Yelwa; Mansur Isah Buhari; Grace Malgwi

Illustration from International Illustration:The Art of Reading 3.0 Copyright: SIL International 2009



Akwai wani yaro mai suna Baƙo.
Baƙo ba ya da tausayi.
Yana son wasan banza.



Wata rana Baƙo ya ga wani makaho.
Makaho ya ɓata hanyar gida.
Makaho ya roƙi Baƙo ya taimake shi.



Baƙo ya kama sandar makaho.
Ya kai makaho cikin daji.
Baƙo ya gudu ya bar makaho.



Ashe baban Baƙo ya gan shi.

Baban Baƙo ya kai makaho gida.



Baba ya dawo gida.
Ya kira Bako.
Ya ce su tafi yawo a daji.



Baƙo da Baba sun shiga daji.
Baba ya ce su yi wasan ɓoye-ɓoye



Baba ya ce Baƙo ya rufe idanunsa.
Baba ya hau bishiya ya ɓ oye.



Baƙo ya buɗe idanunsa.
Baƙo ya fara neman Baba.



Baƙo ya yi sama da ƙasa.
Bai ga Babansa ba.
Baƙo ya fara kuka.
Ya ɓata hanyar gida.



Baba ya sauko daga bishiya.
Baba da Baƙo sun koma gida.
Baƙo ya daina wasan banza.

ALL CHILDREN READING: A GRAND CHALLENGE FOR DEVELOPMENT

USAID FROM THE AMERICAN PEOPLE

World Vision

Australian Aid

GLOBAL READING NETWORK